# Hanya Zuwa ga Allah





Bible text is from the Bible in Hausa, *Littafi Mai Tsarki*, © 1979 by the United Bible Societies, Africa Regional Centre, Nairobi, Kenya. Used by permission.

# ALLAH YA HALICCI DUNIYA TARE DA MASU RAI DUKA



**A sa'ad da Allah ya fara halittar sama da duniya.**

–Farawa 1:1

**Don ta gare shi ne aka halicci dukkan kome, abubuwan da ke sama da abubuwan da ke ƙasa....**

–Kolosiyawa 1:16

**Ubangiji, wanda ya yi sama da ƙasa ya sa muku albarka! Samaniya ta Ubangiji ce kaɗai, amma ya ba mutane duniya.**

–Zabura 115:15, 16

Lokacin da Allah ya halicci duniya ba ta da aibi. Karanta littafin nan domin ka ga abin da ya faru.

# ALLAH YA HALICCI MUTANE



**Allah kuma ya ce, "Bari mu yi mutum cikin siffarmu, da kamanninmu, su mallaki...dukan duniya...."** –Farawa 1:26

# MUTUM YA ZAMA RAYAYYAN TALIKI 

**Sa'an nan Ubangiji Allah ya siffata mutum daga turɓayar ƙasa, a cikin kafafen hancinsa kuwa ya hura numfashin rai, mutum kuma ya zama rayayyan taliki.*** —Farawa 2:7

**Sa'an nan sai Ubangiji Allah ya ce, "Bai kyautu mutumin ya zauna shi kaɗai ba, zan yi masa mataimakin. . . ." Sai Ubangiji Allah ya sa barci mai nauyi ya kwashe mutumin. Lokacin da yake barci Ubangiji Allah ya cire ɗaya daga cikin haƙarƙarinsa ya cike wurin da nama, haƙarƙarin nan kuwa da Ubangiji Allah ya cire daga mutumin ya yi mace da shi, ya kuwa kawo ta ga mutumin.** —Farawa 2:18, 21, 22

*Ma'anar rayayyan taliki shi ne, za mu zauna wani wuri har abada.

4

# ADAMU DA HAWWA'U SUKA YI RASHIN BIYAYYA GA ALLAH



Bai kamata mu ƙasa kunne ga muryar Shaiɗan ba.

Ubangiji Allah ya ɗauki mutumin ya zaunar da shi cikin gonar Aidan ya noma ta, ya kiyaye ta. Ubangiji Allah ya yi wa mutumin umarni, ya ce, "Kana da 'yanci ka ci daga kowane itace da ke gonar, amma daga itacen sanin nagarta da mugunta ba za ka ci ba, gama a ranar da ka ci shi za ka mutu lalle." –Farawa 2:15-17

## SHI MACIJI, WANDA ANA CE DA SHI IBLIS KO SHAIƊAN, YA YI SHAKAR IKON ALLAH, YA YI KARYA.

Amma macijin ya ce wa matar, "Hakika ba za ku mutu ba." Matar ta ga yadda itacen yana da kyau, 'ya'yansa kuma kyawawa, abin sha'awa ne kuma ga ido, abin marmari ne domin ba da hikima, ta tsinka...ta kuwa ci, ta kuma bai wa mijinta...shi kuma ya ci. –Farawa 3:4, 6

# 6 BA SHI YIWUWA ADAMU DA HAWWA'U SU KARA ZAMA CIKIN GONAR AIDAN BA



...Ubangiji Allah ya fisshe shi daga cikin gonar Aidan, ya noma ƙasa, wato inda aka ɗauko shi....Ya kafa kerubobi, da kuma takobi mai harshen wuta...su tsare hanya zuwa itacen rai.

–Farawa 3:23, 24

# RANAR BAKIN CIKI NE KWARAI GA HALITTAR ALLAH DUKA, RAN DA ADAMU DA HAWWA'U SUKA YI ZUNUBI





**. . . Kamar yadda zunubi ya shigo duniya ta dalilin mutum ɗaya, zunubi kuwa shi ya jawo mutuwa, ta haka mutuwa ta zama gādo ga kowa . . . .**

—Romawa 5:12

**Abin Tunawa**

**An haifi kowane mutum da halin zunubi, don haka dukan mutane za su mutu domin zunubi ya kawo mutuwa.** (Karanta Romawa 5:12 kuma.)

# 8 HANYA DA ALLAH YA YI DON YA CECI MUTANE DAGA ZUNUBANSU SHI NE YA AIKO MAKAƊAICIN ƊANSA CIKIN DUNIYA



**"Za ta haifi ɗa, za ka kuma sa masa suna YESU, domin shi ne zai ceci mutanensa daga zunubansu."** –Matiyu 1:21

**Don a shiga cikin 'yan Adamu dole ne a haifi Ɗan Mutum cikin jiki kamar sauran mutane.**

**Domin a cikinsa** [Kristi Yesu] **ne cikin jiki dukkan cikar allahntaka ke tabbata.** –Kolosiyawa 2:9

**Tun fil azal akwai Kalma, Kalman nan kuwa tare da Allah yake, Kalman nan kuwa Allah ne. Kalman nan kuwa ya zama mutum, ya zauna a cikinmu....** –Yahaya 1:1, 14

**An yi wannan ne duk don a cika abin da Ubangiji ya faɗa.... "Ga shi, budurwa za ta yi juna biyu, ta haifi ɗa, za a kuma sa masa suna Immanuwel." (Ma'anar Immanuwel kuwa, Allah na tare da mu.)** –Matiyu 1:22, 23

**Ga shi, an haifa mana ɗa! Mun sami yaro! Shi zai zama Mai Mulkinmu. Za a kira shi, "Mashawarci Mai Al'ajabi, Allah Maɗaukaki, Uba Madawwami, Sarkin Salama."** –Ishaya 9:6

# YESU KRISTI – HADAYA MARA AIBI

**Shi da bai san zunubi ba....** –2 Korantiyawa 5:21



**Bai taɓa yin laifi ba....**
–1 Bitrus 2:22

Babu wata hadaya da mutum ya iya yi da ta isa ta wanki zunubai.

**Domin ba mai yiwuwa ba ne jinin bijimai da na awaki ya ɗauke zunubi.** –Ibraniyawa 10:4

Yesu shi ne Ɗan Rago na Allah. **"Kun ga, ga Ɗan Rago na Allah, mai ɗauke zunubin duniya!"** –Yahaya 1:29b

## YESU YA BA DA RANSA DON YA CECE MU 

An sa Yesu a giciye don miyagun mutane suka ƙi shi, amma mutuwarsa ita ce hanya da Allah ya shirya. Yesu da nufin kansa ya ba da ransa don ya cece ni da kai daga zunubanmu.

Yesu ya ce, **"Ba mai karɓe mini rai, don kaina nake ba da shi. Ina da ikon ba da shi, ina da ikon ɗauko shi kuma...."**
—Yahaya 10:18

### AN FANSHE MU DA JININ YESU ƊAN RAGO NA ALLAH

**...An fanshe ku..., ba da abubuwa masu lalacewa ba kamar azurfa da zinariya, sai dai da jinin nan mai daraja na Almasihu, kamar na ɗan rago marar naƙasa, marar tabo.** —1 Bitrus 1:18, 19

### BABU WATA HADAYA DA TA ISA TA WANKI ZUNUBAI

**...Aka tsarkake mu, ta wurin miƙa jikin Yesu Almasihu hadaya sau ɗaya tak ba ƙari.** —Ibraniyawa 10:10

**12 ...Tun da ya ke yanzu an kuɓutar** [maida mu mara laifi] **da mu ta jininsa,...ta wurinsa za mu fi samun kārewa daga fushin Allah ke nan.**
—Romawa 5:9




**"...Tun muna masu zunubi** [masu rashin biyayya ga Allah] **Almasihu ya mutu dominmu."**
—Romawa 5:8

# DUK MASU GASKATA DA YESU ƊAN ALLAH SUKE DA RAI MADAWWAMI



"Saboda ƙaunar da Allah
ya yi wa duniya har ya ba da
makaɗaicin Ɗansa, domin
duk wanda ya gaskata da
shi kada ya halaka, sai dai
ya sami rai madawwami."
–Yahaya 3:16

**Ya tsamo mu daga mulkin duhu, ya maishe mu ga mulkin ƙaunataccen Ɗansa, wanda ta gare shi ne muka sami fansa,* wato gafarar zunubanmu.** –Kolosiyawa 1:13, 14

*Ma'anar fansa shi ne an saye mu kuma.

# "YA TASHI!"



Amma sai mala'ikan ya ce wa matan, "Kada ku ji tsoro, domin na sani Yesu kuke nema, wanda aka gicciye. Ai, ba ya nan. Ya tashi, yadda ya faɗa. Ku zo ku ga wurin da aka sa shi."

—Matiyu 28:5, 6

**Ni ne kuma Rayayye. Dā na mutu, amma ga shi yanzu, ina raye har abada abadin, ina kuwa da mabuɗan mutuwa da na Hades** [Jahanama]. —Wahayin Yahaya 1:18

**"...Saboda ni a raye nake, ku ma za ku rayu."** —Yahaya 14:19

Da shi ke Yesu ya yi nasara da mutuwa, yana da mabuɗin mutuwa, ba dalili mu ji tsoron mutuwa ba.

**Sa'ad da nake jin tsoro, ya Maɗaukaki, a gare ka nake dogara.** —Zabura 56:3

(Duba shafi 46 ka ga alƙawarin Allah.)

## YESU YA IYA CECE KA, YANA ADDU'A DOMIN KA

**Amma shi da ya ke madawwami ne....Yana da ikon ceton masu kusatowa ga Allah ta wurinsa, matuƙar ceto, tun da ya ke kullum a raye yake saboda yi musu addu'a.** —Ibraniyawa 7:24, 25

# DA NI DA KAI MUN IYA SAMUN RAI MADAWWAMI




**Wace ƙanya KA ke bi?**

Yesu Kristi shi ne HANYA zuwa RAI madawammi wurin Allah.

Shaiɗan shi ne hanya zuwa MUTUWA na har abada.

Wannan yaro ya zaɓi rai madawwami.

**"...Yau sai ku zaɓi wanda za ku bauta wa...."** –Joshuwa 24:15

**"...Ku zaɓi rai fa, don ku rayu, ku da zuriyarku."**
–Maimaitawar Shari'a 30:19

## YESU SHI NE HANYA ZUWA RAI MADAWWAMI

**"Ba kuma samun ceto ga wani, domin ba wani suna duk duniyan nan da aka bayar cikin mutane, wanda lalle ta wurinsa ne za mu sami ceto."** –Ayyukan Manzanni 4:12

**"Ni kaɗai ne Ubangiji, Ni kaɗai ne wanda yake da ikon yin ceto."**
–Ishaya 43:11

# 18 DON ME YA ZAMA DOLE MU ZAƁI YESU IDAN MUNA SO RAI MADAWWAMI?

**1. *Yesu ne ya zo.***

**"...Ni kuwa na zo ne domin su sami rai...."**

–Yahaya 10:10



**2. *Yesu ne ya ƙamnace mu, ya ba da ransa dominmu.***

**...Ɗan Allah,...ya ƙaunace ni, har ya ba da kansa domina.**

–Galatiyawa 2:20

Yesu ya zama mutum da tsoka da jini kamarmu,...**domin ya hallakar da mai ikon mutuwa, wato Iblis,**

**ta mutuwarsa, yă kuma 'yanta duk wadanda tun haihuwarsu suke zaman bauta saboda tsoron mutuwa.**
–Ibraniyawa 2:14, 15

**3.** ***Jinin Yesu kadai ya zama maganin zunubanmu.***

**...Gama da jini ake kafara** [gafara] **saboda akwai rai a cikinsa.**
–Littafin Firistoci 17:11

**...Jinin Yesu Ɗansa kuma yana tsarkake mu daga dukkan zunubi.**
–1 Yahaya 1:7

**Wanda ta gare shi ne muka sami fansa, wato gafarar zunubanmu.**
–Kolosiyawa 1:14



### 4. *Yesu Kristi ya tashi daga matattu.*

**Mun sani tun da ya ke an ta da Almasihu daga matattu, ba zai sāke mutuwa ba ke nan, mutuwa ba ta da sauran wani iko a kansa.** –Romawa 6:9

**Ya kuwa mutu ne saboda dukan mutane, domin waɗanda ke raye, kada su yi zaman ganin dama nan gaba, sai dai su yi zaman wannan da ya mutu saboda su, aka kuma tashe shi saboda su.** –2 Korantiyawa 5:15

Yesu ya ce, "**...Saboda ni a raye nake, ku ma za ku rayu.**"
–Yahaya 14:19

**5.** ***Dole ne muna da Ruhun Kristi cikinmu don a tashe mu zuwa ga rai madawwami (rai na har abada).***



**...Almasihu a cikinku, sa zuciyar ɗaukakar da za a bayyana.** –Kolosiyawa 1:27

**In kuwa Ruhun wannan da ya ta da Yesu daga matattu na zaune a zuciyarku, to, shi da ya ta da Almasihu Yesu daga matattu zai kuma raya jikin nan naku mai mutuwa, ta Ruhunsa da ke zaune a zuciyarku.** –Romawa 8:11

**KA TABBATA RUHUN KRISTI YANA ZAMNE A CIKIN KA**

**...Duk wanda ba shi da Ruhun Almasihu kuwa, ba na Almasihu ba ne.** –Romawa 8:9

# GA YADDA KA IYA SAMUN RAI MADAWWAMI

Ka duba shafi 24. Bi dokoki a wurin.



**Ayyukan da saurayi ke yi suke bayyana yadda yake....**
–Karin Magana 20:11

"Yesu yana ƙamnata, na tabbata, gama Littafi Mai Tsarki ya gaya mani haka."

**Amma Yesu ya kira 'yan yara wurinsa ya ce, "Ku bar yara ƙanana su zo wurina, kada ku hana su. Ai, Mulkin Allah na irinsu ne."** –Luka 18:16

**"Haka ma, ba nufin Ubanku da ke cikin Sama ba ne ɗaya daga cikin waɗannan 'yan yara ya halaka."** –Matiyu 18:14

Ba kome ko kai wanene ne ko inda ka ke zauna, Yesu ya ƙaunace ka, ya mutu dominka. Yesu yake so ka ƙaunace shi kuma. Ka iya nuna masa ƙaunarka ta wurin yi masa biyayya.

**"In dai kuna ƙaunata, za ku bi umarnina."** –Yahaya 14:15

# HANYAR ALLAH TA SAMUN RAI MADAWWAMI

1. ***Ka yarda kai mai zunubi ne. (Ka yi wa Allah rashin biyayya.)***

**Gama 'yan adam duka sun yi zunubi, sun kasa kuma ga ɗaukakar Allah.**

–Romawa 3:23

2. ***Ka zo wurin Allah, ta wurin Yesu.***

**Domin Allah ɗaya ne, matsakanci kuma ɗaya ne tsakanin Allah da mutane–Almasihu Yesu, mutum.**

–1 Timoti 2:5

**Saboda haka yana** [Yesu] **da ikon ceton masu kusatowa ga Allah ta wurinsa, matuƙar ceto....**

–Ibraniyawa 7:25

Yesu ya ce, **"...Wanda kuwa ya zo gare ni ba zan kore shi ba ko kaɗan."**

–Yahaya 6:37

**3.** ***Ka yi tuba na zunubanka.***

(Ma'anar tuba ita ce ka yi baƙin ciki domin zunubanka har ka daina yin su.)

**Saboda haka sai ku tuba, ku juyo, domin a shafe zunubanku....**

–Ayyukan Manzanni 3:19

**Ubangiji...mai haƙuri ne gare ku, ba ya so kowa ya halaka, sai dai kowa ya kai ga tuba.** –2 Bitrus 3:9




**4.** ***Ka bayyana wa Yesu zunubanka.***

**26** Ka rubuta 1 Yahaya 1:9 a nan daidai yadda yake a cikin hannu shafi 25.

________________________________________________

________________________________________________

________________________________________________

________________________________________________

**5. *Rabu da zunubanka.***
(Ma'anar rabu da su ita ce ka daina yin su.)

**Ba za ka taɓa cin nasara a zamanka ba muddin kana ɓoye laifofinka. Ka hurta zunubanka ka tuba, sa'an nan Allah zai yi maka jinƙai.** —Karin Magana 28:13

**Ka rabu da mugunta ka aikata nagarta. . . .** —Zabura 37:27

## 6. *Ka gaskata da Yesu.*



**Domin ta wurin alheri ne aka cece ku saboda bangaskiya, . . . baiwa ce ta Allah, ba kuwa saboda aikin lada ba, kada wani ya yi fariya.** –Afisawa 2:8, 9

**. . . In kai da bakinka ka bayyana yarda, cewa Yesu Ubangiji ne, ka kuma gaskata a zuciyarka Allah ya tashe shi daga matattu, za ka sami ceto.** –Romawa 10:9

**". . . Ka gaskata da Ubangiji Yesu, za ka sami ceto, kai da iyalinka."** –Ayyukan Manzanni 16:31

## 7. *Ka Karɓa Yesu Kristi cikin zuciyarka da ranka.*

Kai kaɗai ka iya buɗe ƙofar zuciyarka, ka roƙe Yesu ya shiga cikinta. Yesu ya ce, **"Ga ni nan tsaye a bakin ƙofa, ina ƙwanƙwasawa, kowa ya ji muryata ya buɗe ƙofar, sai in shiga wurinsa, in ci abinci tare da shi, shi kuma tare da ni."**

–Wahayin Yahaya 3:20



**Amma duk iyakar waɗanda suka karɓe shi, wato masu gaskatawa da sunansa, ya ba su ikon zama 'ya'yan Allah.**

–Yahaya 1:12

# GA ADDU'A DA KA IYA YI



Idan ba ka taɓa yi addu'a ba, amma kana so a taimake ka ka yi addu'a wannan zai zama maka taimako:



**Ya Ubangiji Yesu,**

**Na gode maka don ka mutu bisa giciye sabili da zunubana. Na yi baƙin ciki don laifofina da zunubai duka da na yi. Ina roƙonka ka shiga zuciyata, ka zauna cikina har abada. Ina dogara gare ka ka tsarkake zuciyata. Na karɓe ka ka zama mai cetona da Ubangijina.**

**Cikin sunan Yesu Kristi, Amin.**

# 30 IDAN YESU YANA CIKIN ZUCIYARKA KANA DA RAI MADAWWAMI

**...Allah yā ba mu rai madawwami, wannan rai kuwa yana cikin Kansa. Duk wanda ke da Ɗan, yana da rai....**

—1 Yahaya 5:11, 12

**...Duk mai jin maganata, yake kuma gaskata wanda ya aiko ni...ya tsere wa mutuwa, ya kai ga rai.** —Yahaya 5:24

Sa'anda jikinka ya mutu, kana tare da Ubangiji (2 Korintiyawa 5:8). **...Almasihu a cikinku, sa zuciyar ɗaukakar da za a bayyana.**

—Kolosiyawa 1:27

Idan ka roƙi Yesu shi gafarta maka zunubanka, ka gaskata Yesu Kristi Ubangiji ya zama Mai Cetonka, ka rubuta sunanka nan:



Ka karanta ayoyi daga cikin Littafi Mai Tsarki (Maganar Allah) kowace rana, ka ɓoye su cikin zuciyarka, ka haddace su waɗanda suna da ma'ana a gareka. (Akwai su da yawa cikin wannan ɗan littafi.)

**Kowane Nassi hurarre na Allah ne, mai amfani ne kuma wajen koyarwa, da tsawatarwa, da gyaran hali, da kuma tarbiyyar aikin adalci.**

–2 Timoti 3:16

# KA YI MAGANA DA YESU CIKIN ADDU'A KOWANE LOKACI



Ka *yi masa godiya* domin dukan abubuwa masu kyau da ya yi maka a wannan rai. Ka *yabe shi* domin dukan abin da ya yi maka, da kuma domin cetonka. Ka *yi* masa *addu'a domin kowace bukata da kake da shi.* Yi addu'a cikin sunansa.

**...In mun roƙi kome bisa ga nufinsa, sai ya saurare mu.** –1 Yahaya 5:14

**...Kome kuka roƙi Uba zai ba ku saboda sunana.** –Yahaya 16:23

**...Kuna yi wa juna addu'a....** –Yakuba 5:16

**...Ku yi wa masu tsananta muku addu'a.** –Matiyu 5:44

# ADDU'A DA YESU YA KOYA WA ALMAJIRANSA SU YI



(Almajiri mutum ne wanda yake bin Yesu.)

Yesu ya gaya musu su yi addu'a kamar haka:

**"...Ya Ubanmu wanda ke cikin Sama, A kiyaye sunanka da tsarki. Mulkinka yǎ zo, A aikata nufinka a duniya kamar yadda ake yi a Sama. Ka ba mu abincinmu na yau. Ka gafarta mana laifofinmu, Kamar yadda mu ma muke gafarta wa waɗanda ke yi mana laifi. Kada ka kai mu wurin jaraba, Amma ka cece mu daga Mugun."** –Matiyu 6:9-13

Ya kamata a haddaci wannan addu'a, domin masu bi su kan yi wannan addu'a tare da murya.

# 34 DOKOKI GOMA NA ALLAH SUKE KOYA MANA YADDA YA KAMATA MU YI RAYUWARMU

(Fitowa 20)

***Su huɗu na fari suke koya mana batun ƙamnarmu zuwa ga Allah***

1. Kada ka kasance da waɗansu alloli sai ni.
2. Kada ka yi wa kanka wani gunki ko kuwa wata siffa ta wani abu.... Kada ka rusuna musu, kada kuwa ka bauta musu.
3. Kada ka kama sunan Ubangiji Allahnka a banza.
4. Tuna da rana Asabar, ka kiyaye ta da tsarki.

***Sauran su shidda suke koya mana batun ƙamnarmu zuwa ga mutane***

5. Ka girmama mahaifinka da mahaifiyarka.
6. Kada ka yi kisankai.
7. Kada ka yi zina.
8. Kada ka yi sata.
9. Kada ka ɓāta sunan maƙwabcinka.
10. Kada ka yi ƙyashin.

## BIYAYYA GA ALLAH YA KAN KAWO AMSOSHIN ADDU'ARMU

Mukan kuwa sami duk abin da muka roƙa a gare shi, domin muna bin umarninsa, muna kuma yin abin da yake so.

—1 Yahaya 3:22

# DOKOKI BIYU MASU FI GIRMA

## Kamna ga Allah

**1. Ya ce masa, "Ka ƙaunaci Ubangiji Allahnka da dukkan zuciyarka, da dukkan ranka, da dukkan hankalinka. Wannan shi ne babban umarni na farko."** –Matiyu 22:37, 38

## Kamna ga Mutane

**2. "Na biyu kuma kamarsa yake, 'Ka ƙaunaci ɗan'uwanka kamar kanka.'"**

–Matiyu 22:39




Dukan dokoki goma ɗin an tara su cikin dokoki biyu nan masu fi girma. (Shafi 34 da 35.)

# KAMNA TA FI SU DUKA GIRMA



**Sura na ƙamna**

(1 Korintiyawa 13:1-8, 13)

**[1]Ko da zan yi magana da harsunan mutane, har da na
mala'iku, amma ya zamana ba ni da ƙauna, na zama ƙararrawa
mai yawan ƙara ke nan, ko kuge mai amo. [2]Ko da zan yi
annabci, ina kuma fahimtar dukkan asirai, da dukkan ilimi, ko
da kuma ina da matuƙar bangaskiya har yadda zan iya kawar
da duwatsu, muddin ba ni da ƙauna, to, ni ba kome ba ne. [3]Ko
da zan sadaukar da duk abin da na mallaka, in kuma ba da
jikina a ƙone, in har ba ni da ƙauna, to, ban amfana da kome
ba. [4]Kauna tana sa haƙuri da kirki. Kauna ba ta sa kishi, ba ta
yin kumbura. [5]Kauna ba ta sa ɗaga kai ko rashin kārā, ƙauna
ba ta sa sonkai, ba ta jin tsokana, ba ta riƙo. [6]Kauna ba ta sa**

yin farin ciki da mugunta, sai dai da gaskiya. [7]Kauna tana sa
daurewa cikin kowane hali, da bangaskiya cikin kowane hali,
haka kuma sa zuciya cikin kowane hali, da jimiri cikin kowane
hali. [8]Kauna ba ta ƙarewa har abada. Annabci zai shuɗe,
harsuna za su ɓace, ilimi kuma zai shafe.
[13]To, yanzu abubuwan nan uku sun tabbata, bangaskiya, da
sa zuciya, da kuma ƙauna, amma duk mafi girma a cikinsu ita
ce ƙauna.

## ALLAH KAMNA NE

. . . Allah shi ne ƙauna, wanda ke a dawwame cikin ƙauna kuwa, ya dawwama a cikin Allah ke nan, Allah kuma a cikinsa.

–1 Yahaya 4:16



(a gida, a makaranta, a majami'a, da koina)

Yesu ya ce, **"Tafi gida wurin 'yan'uwanka, ka faɗa musu irin manyan abubuwan da Ubangiji ya yi maka, da kuma yadda ya ji tausayinka."**

–Markus 5:19b

# YADDA ZA A SAN 'YA'YAN ALLAH NA GASKIYA

**Don haka da irin aikinsu za ku gane su.** –Matiyu 7:20

**Albarkar Ruhu kuwa ita ce ƙauna, da farin ciki, da salama, da haƙuri, da kirki, da nagarta, da aminci, da tawali'u da kuma kamunkai. . . .** –Galatiyawa 5:22, 23

## MAI BI NA GASKIYA YA KAN GAFARTA MA WASU

**Domin in kun yafe wa mutane laifofinsu, Ubanku na Sama zai yafe muku.** –Matiyu 6:14

## ABU BAKWAI DA ALLAH YA KI

**Duban raini, harshe mai faɗar ƙarya, hannuwan da ke kashe marasa laifi, kwanyar da ke tunane-tunanen mugayen dabaru, mutum mai gaggawar aikata mugunta, mai yawan shaidar zur, mutum mai ta da fitina a tsakanin abokai.** –Karin Magana 6:17-19




## AIKIN HALIN MUTUNTAKA: 41

...Fasikanci, da aikin lalata, ...da bautar gumaka, da sihiri, da gāba, ...da kishi, da fushi, ...da hassada, da buguwa, da shashanci, da kuma sauran irinsu.... Masu yin irin waɗannan abubuwa ba za su sami gādo a Mulkin Allah ba. –Galatiyawa 5:19-21

...Ko masu luɗu da maɗugo, ko ɓarayi, ko makwaɗaita.... –1 Korantiyawa 6:9, 10

## BAR YESU YA CIKA KA DA RUHUNSA, YA TSARKAKE KA

Waɗansunku ma dā haka suke, amma an wanke ku, an tsarkake ku, ...da sunan Ubangiji Yesu Almasihu, da kuma Ruhun Allahnmu. 1 Korantiyawa 6:11

# 42 JAHANNAMA TABBATACIN WURI NE




(Karanta Luka 16:19-26.)

Sai ka tabbata kake dogara ga Yesu. Zai rubuta sunanka cikin Littafin Rai.

**Duk wanda ba a sami sunansa a rubuuce a Littafin Rai ba, sai a jefa shi a tafkin nan na wuta.**
–Wahayin Yahaya 20:15

...Allah yā ba mu rai madawwami, wannan rai kuwa yana cikin Ƙansa.
—1 Yahaya 5:11

Gama sakamakon zunubi mutuwa ne, amma baiwar Allah ita ce rai madawwami cikin Almasihu Yesu Ubangijinmu.
—Romawa 6:23

"Wanda ya gaskata da Ɗan, yana da rai madawwami. Wanda ya ƙi bin Ɗan kuwa, ba zai sami rai ba, sai dai fushin Allah ya tabbata a gare shi."
—Yahaya 3:36

Yesu ya ce masa, "Ni ne hanya, ni ne gaskiya, ni ne kuma rai. Ba mai zuwa wurin Uba sai ta wurina."
—Yahaya 14:6

# 44 SAMA (GIDAN ALLAH) TABBATACIN WURI NE



Cikin wahayin Yahaya (Wahayin Yahaya 21) ya ce ya ga sabuwar sama da sabuwar ƙasa.

**"Zai share musu dukkan hawaye. Ba kuma sauran mutuwa, ko baƙin ciki, ko kuka, ko azaba, don abubuwan dā sun wuce." Sai na zaune a kan kursiyin ya ce, "Kun ga, ina yin kome sabo."...**
–Wahayin Yahaya 21:4, 5

Yahaya ya ga tsattsarkan birni da sabuwar Urushalima suna saukowa daga sama wurin Allah. "...**Birnin kuma da zinariya zalla, garau kamar ƙarau. An kuma ƙawata harsasan garun birnin da kowane irin dutse mai daraja....**"
–Wahayin Yahaya 21:18, 19

# YESU YA TAFI DON YA SHIRYA WURI
# DOMIN DUKA WAƊANDA SUKA GASKATA DA SHI

"Kaɗa ku damu. Ku gaskata da Allah, ku kuma gaskata da ni. A gun Ubana akwai wurin zama da yawa. Da ba haka ne ba, da na faɗa muku, domin zan tafi in shirya muku wuri. In kuwa na je na shirya muku wuri, sai in dawo in kai ku wurina, domin inda nake, ku ma ku zama kuna can." –Yahaya 14:1-3

## KA SHAIDA MA WASU LABARI MAI DAƊIN NAN

Yesu ya ce, **"Ku tafi ko'ina a duniya, ku yi wa dukkan 'yan adam bishara."** –Markus 16:15

**...Wanda yake da hikima kuma yakan ceci rayuka.**

–Karin Magana 11:30

# 46 ALKAWARIN ALLAH GA 'YA'YANSA

"...Har abada ba zan bar ka ba. Har abada kuma ba zan yashe ka ba." —Ibraniyawa 13:5

Allah zai sa mala'ikunsa su lura da kai, za su kiyaye ka duk inda za ka tafi. —Zabura 91:11



"...Ba kuwa mai iya ƙwace su daga ikon Uban." —Yahaya 10:29

"...Ga shi, ni kuma kullum ina tare da ku har matuƙar zamani." —Matiyu 28:20

"Kada ka ji tsoron wuyar da za ka sha....Ka riƙi amana ko da za a kashe ka, ni kuwa zan ba ka kambin rai." —Wahayin Yahaya 2:10

...Sa'ad da na zauna cikin duhu, Ubangiji zai haskaka ni. —Mika 7:8

"Ka kira ni, ni kuwa zan amsa maka...." —Irmiya 33:3

# YESU YANA ZUWA KUMA 

Za a ta da kowane mutum daga matattu.

**"...Lokaci na zuwa da duk waɗanda ke kaburbura za su ji murya tasa, su kuma fito, waɗanda suka aikata nagarta su tashi, tashin rai, waɗanda suka yi rashin gaskiya kuwa su tashi, tashin hukunci."**

–Yahaya 5:28, 29



Waɗanda suka mutu suna na Almasihu za su fara tashi.

**"Sa'an nan sai mu da muka wanzu, muke raye, za a ɗauke mu tare da su ta cikin gajimare, mu sadu da Ubangiji a sararin sama, sai kuma kullum mu kasance tare da Ubangiji."**

–1 Tasalonikawa 4:17

**"...Ku zauna a faɗake, kuna addu'a, domin ba ku san sa'ar da lokacin zai yi ba."**

–Markus 13:33

# 48 YAYA YESU ZAI DAWO?



**Ga shi, zai zo a cikin gajimare, kowa zai gan shi. . . .** –Wahayin Yahaya 1:7

Yi hankali da almasihan ƙarya da annabawan ƙarya.

**". . . In kowa ya ce muku, 'Kun ga, ga Almasihu nan!' ko, 'Ga shi can!' kada ku yarda. . . . In sun ce da ku, 'Ga shi can a jeji,' kada ku fita. In kuwa sun ce, 'Yana can cikin loloki,' kada ku yarda."**
–Matiyu 24:23, 26

## YESU ZAI ZO DA SAURI CIKIN GAJIMAREN SAMA

**"Kamar yadda walƙiya take wulgawa walai daga gabas zuwa yamma, haka komowar Ɗan Mutum za ta zama. . . . Duk kabilan duniya . . . za su ga Ɗan Mutum na zuwa kan gajimare, da iko da ɗaukaka mai yawa."** –Matiyu 24:27, 30

# ZABURA NA MAKIYAYI

(Zabura 23)

**1 Ubangiji makiyayina ne, Ba zan rasa kome ba.** 2 Yana sa
ni in huta a saura mai ɗanyar ciyawa, Yana bi da ni a tafkuna
masu daɗin ruwa, suna kwance lif. 3 Yana ba ni sabon ƙarfi.
Yana bi da ni a hanyar da ke daidai kamar yadda ya
alkawarta.

**4 Ko da hanyan nan ta bi ta tsakiyar duhu na mutuwa,**
**Ba zan ji tsoro ba, ya Ubangiji, Gama kana tare da ni!**
**Sandanka na makiyayi da kerenka suna kiyaye lafiyata.**
5 Ka shirya mini liyafa Inda maƙiyana duk za su iya ganina, Ka
marabce ni, ka shafe kaina da mai, ka cika tanduna fal da
mai.

**6 Hakika, alherinka da ƙaunarka, za su kasance tare da**
**ni muddin raina. Haikalinka zai zama gidana har abada.**

new 6/94

Idan kake so ka karɓa wasu ɗan littatafai na koyarwar Maganar Allah sai ka rubuta wa wanda ya yi su.

**World Missionary Press, Inc.**
**P.O. Box 120**
**New Paris, Indiana 46553-0120 U.S.A.**

Hausa Nigeria



Wannan kyauta ce–Ba don sayarwa ba ne.

2210 Hausa WTG